# MAFARKIN FIR'AUNA

(Hausa)

MUHAMMAD ILYAS
Attar Qadiri Razavi

**Mafarkin Fir'auna**

Fassarar Hausa ta 'Fir'awn kā Khuwāb'

⟐

**DUKKANIN HAKKI TSARARRENE**

Copyright © 2025 Maktaba-tul-Madinah

---

Ba'a yarda a sauya ko a buga ko a sadar dashi ta kowace hanya ba koda ta hanyar photo copy ne batare da rubutaccen izini ba daga Maktaba-tul-Madinah.

| | |
|---|---|
| **Bugu na 2:** | Ramadan-ul-Mubarak, 1446 AH (March, 2025) |
| **Madaba'a:** | Maktaba-tul-Madinah |
| **Adadi:** | 4000 |

---

## Du'ā for Reading the Book

Karanta wannan Addu'a kafin ka fara Nazarin Littatafan musulunci ko karantawa اِنْ شَآءَاللّٰہعَزَّوَجَلَّ. Zaka Rike duk abinda karanta

اَللّٰهُمَّ افْتَحْ عَلَيْنَا حِكْمَتَكَ وَانْشُرْ
عَلَيْنَا رَحْمَتَكَ يَـا ذَاالْجَلَالِ وَالْاِكْرَام

**Fassara:** Ya ubangijina Allah عَزَّوَجَلَّ! Ka budemana kofofin Ilimi da Hakima Kaji kanmu ya mafi girma da daukaka *(Al-Mustaṭraf, mujallad. 1, shafi. 40)*

**tunatarwa: ka kar ka mata dayiwa Annabi** ﷺ a farko da karshe Bayan gama addu'a

فِرعون کا خُواب

Fir’awnkāKhuwāb

# MAFARKIN FIR’AUNA

Wannan karamin Littafi Sheikun Darika, Amiru ahlul Sunnah, Shugaban Kungiyar Dawatul Islami ‘Babban Malami Abu Bilal Muhammad Ilyas Attar Qadiri Razavi دَامَتۡ بَرَکَاتُہُمُ الۡعَالِیَہ a yaren Urdu. **Sashen Masu fassara suka fassarashi zuwa hausa**.idan an samu ganin kuskure a fassarar ko wajen rubutun to asanar da Sashen masu fassara ta wadannan hanyoyi ko hanyar aikawa ta akwatin sako ko kuma ta adireshin email da niyyar samin lada.

**Translation Department (Dawat-e-Islami)**

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagran, Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan

**UAN:**☎ +92-21-111-25-26-92 – Ext. 7213

**Email:** translation@dawateislami.net

# Transliteration Chart

| | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|
| ء | A/a | ڑ- | Ř/ř | ل | L/l |
| ا | A/a | ز | Z/z | م | M/m |
| ب | B/b | ژ | X/x | ن | N/n |
| پ | P/p | س | S/s | و | V/v, |
| ت | T/t | ش | Sh/sh | | W/w |
| ٹ | Ṫ/ṫ | ص | Ṣ/ṣ | ھ/ ہ /ۃ | Ĥ/ĥ |
| ث | Š/š | ض | Ḍ/ḍ | ی | Y/y |
| ج | J/j | ط | Ṭ/ṭ | ے | Y/y |
| چ | Ch | ظ | Ẓ/ẓ | ◌َ | A/a |
| ح | Ḥ/ḥ | ع | ‘ | ◌ُ | U/u |
| خ | Kh/kh | غ | Gh/gh | ◌ِ | I/i |
| د | D/d | ف | F/f | ومدّہ | Ū/ū |
| ڈ | Ḋ/ḋ | ق | Q/q | ی مدّہ | Ī/ī |
| ذ | Ż/ż | ك | K/k | امدّہ | Ā/ā |
| ر | R/r | گ | G/g | | |



www.dawateislami.net

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَ الصَّلٰوةُ وَ السَّلَامُ عَلٰی سَيِّدِ الْمُرْسَلِيْنَ
اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ ؕ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ ؕ

# MAFARKIN FIR'AUNA

## Falalar Salati Ga Manzon Allah ﷺ

Annabin Rahma mai Ceton alumma mai kyautar Aljannah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace : 'Dukkan wanda yayi salati a gareni guda daya Allah عَزَّوَجَلَّ Zai yi masa Guda Goma'

*(Muslim, shafi 216, Ḥadisi 408)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد



www.dawateislami.net

## 1. Mafarkin Fir’auna

Wata rana Fir’auna yayi Mafarkin Wuta ta tashi a *Baitul-Mukaddas*, Ta cinye Dukkan Birnin Misra tare da kone Mazauna Garin zuwa toka, Amma kuma Banu Isra’ila sam Babu Abinda ya samesu na daga wannan Wuta data tashi.Ran Fir’auna yayi matukar tashi da wannan Mafarki Rikirkitacce, Sai ya kira Masu duba da taurari su fassara masa mafarkinsa, Sukayi masa Fassarar cewa Za’a haifi wani Yaro a cikin Banu isra’la Wanda zaikawo karshen mulkinka da kuma faduwar wannan kasaitacciyar Daula taka. Daga jin Haka sai Fi"auna yabayar da Umarnin Kashe duk Wani Jariri da aka Haifa daga Banu Isra’ila, Akarkashin Wannan Umarni na Fir’auna an kashe Jarirai kimanin Dubu Ashirin ko Dubu Saba’in a karkashin dokar Fir’auna

*(Tafsīr-e-Khāzin, mujallad. 1, shafi. 52)*

## Menene Sunan Fir'auna na Gaskiya ?

Yaku Yara masu Albarka ! Azamanin da dukkan Sarkin Masar ana kiransa da Fir'auna Hakakuma Sarkin Rome ana kiransa da Qaysar haka kuma Sarkin Iran Ana kiransa da Kisra, Sarkin Yemen kuma shine Tuba Sarkin Turkiya kuma shine Khāqān, kuma Sarkin Habasha/Itopia Anakiransa da Najjāshī. Acikin Fir'aunonin kasar masar na Zamanin Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام Yafi su Rashin Imana da Mugunta da keta kuma Azzalumine Sunansa na Gaskiya shine Walīd Ibn Muṣ'ab Bin Rayyān kuma kuma dan asalin Yaren Coptic Sunan Fir'aunan Zamanin Annabi Yusuf عَلَيْهِ السَّلَام Shine Rayyān Bin Walīd Wanda ya Musulunta daga Baya.

Da akwai Nisan Tazarar Shekaru Fiye da 400 a Takanin Zamanin Annabi Yūsuf Da Annabi Musa عَلَيْهِمُ السَّلَام.

# An Boye Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام Acikin Tanderun Gurasa

## 2. An saka Annabi Mūsā عَلَيْهِ السَّلَام A Cikin Tanderu [Tukunyar kasa ta gasa gurasa]

A daidai Lokacin da Haihuwar Annabi Mūsā Kalamullāĥ’s عَلَيْهِ السَّلَام, ta Matso Fir’auna ya aika Unguwar zoma daga Bani Isra’ila izuwa wajen Mahaifiyarsa رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه. Bayan Haihuwar Annabi Mūsā عَلَيْهِ السَّلَام, sai wani haske yake fita ta tsakanin Idanuwansa, Lokacin da unguwar zoma nan taga wannan haske sai ta rikirkice kuma taji ta kamu da kauna matuka ga Annabi Musa Kalamullāĥ عَلَيْهِ السَّلَام. Unguwar zoman nan tace da Mahaifiyarsa رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه, ‘Nazo ne Musanman domin na kashe Jaririnki idan Namijine to Amma naji ina kaunarsa, Ki boye daga ‘yan aiken Fir’auna Bayan  tagama fadar haka sai ta tafi Tana fitowa sai ‘yan aiken fir’auna  suka lura cewa ta fitone daga gidan sai suka himmatu zuwa kofar gidan ‘yan  leken  asirin Fir’auna sun tsaya a



www.dawateislami.net

kofar gidan sai ga 'yar uwa ga Annabi MūsāKalīmullāĥ عَلَيْهِ السَّلَام, sai taje tasanar wa Mahaifiyar. Annabi Mūsā' رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ita kuma saboda ta tsorata kuma a cikin irin wannan lokaci cikin hanzari sai kawai ta nade Jaririn a cikin wata tufa ta sakashi a cikin Garwashin wutar Tanderun Gasa Gurasa , kuma a daidai wannan lokacine 'yan liken asirin suka shigo gidan , sun bincika ko ina da ko ina amma basu ga wani Jariri ba kuma Hankalin su sam baiyi ta wajen da ake Tanderun gasa gurasa ba daga nan suka fice daga gidan. Mahaifiyarsa رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه Tayi ajiyar Zuciya Haka kuma a take tajiyo shishshikar kuka a hankali tana fitowa daga tukunyar kasa ta gasa Gurasa data duba sai taga Allah عَزَّوَجَلَّ ya mayar da wutar mai sanyi da ni'ima ga Jaririnta ( Sayyidunā Mūsā عَلَيْهِ السَّلَام).Ta fito dashi daga tukunyar Gurasa lafiyarsa garau . *(Tafsīr Baghawī, mujallad. 3, shafi. 373)*



www.dawateislami.net

**carpenter ya zama kurma**

## 3. carpenter ya zama kurma

Mahaifiyar Annabi Musa رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه Ta tafi wajen wani mutum mai aikin carpenter domin siyo akwatin katako. Sai ya tambayeta:’mezakiyi da akwatin katako? Sai ta gayamasa gaskiya cewar ina son na saka dana acikin akwatin katako na kaishi Kogi domin tsira daga mutanen Fir’auna, Duk da mutumin nan ya siyar mata da akwatin katakon nan daga baya kuma sai mugun nufi ya shiga ran sa domin gayawa mutanen Fir’auna dake da alhakin kamawa da kuma kashe duk Jaririn da’aka Haifa idan Namijine a cikin Banī Isrāīl. Yayin daya isa wajensu Sai Allah عَزَّوَجَلَّ Ya Kulle bakinsa sai ya kasa Magana sai dai Ishara irinta kurma yayita kokarin nuna musu cewa Ga wata mata zata saka Jariri a akwatin katako, Mutanen Fir’auna basu gane mai yake nufi ba, sai suka dauko Bulala sukai masa duka

Domin kallon Mahaukaci suke masa shi kuma hakan ya tilasta masa Rugawa da gudu Bayan komawarsa gida kuma sai, Allah عَزَّوَجَلَّ Ya bude masa bakinsa ya koma yana Magana. Daga budewar bakin nan nasa sai ya kuma komawa wajen mutanen Fir’auna Domin sanar dasu, yana zuwa kuwa sai Bakinsa ya kuma kullewa ya kasa Magana da harshensa sai mutanennan suka kara korashi da duka Domin a zatonsu shi mahaukacine bashida hankali, Yana komawa gida sai bakinsa ya bude haka kuma a karo na Uku ya kuma komawa wajen mutanen fir’auna domin sanar dasu yana zuwa kuwa sai bakinsa ya kulle kuma idanunsa suka Makance kuma yaci duka har ya Runtuma a guje Toh! Daya ga haka sai ya Tuba yace: ‘Ya Allah عَزَّوَجَلَّ! Idan ka dawomin da ganina kuma Bakina ya bude Bazan gayawa kowaba akan Jaririn da aka Haifa ba (yana nufin



www.dawateislami.net

Annabi Musā عَلَيْهِ السَّلَام). Allah عَزَّوَجَلَّ Ya karbi Tubansa kuma ya dawo masa da ganinsa haka kuma bakinsa ya bude. *(ibid)*

## Kada mu saurara kukuma mugani kukuma mufadi mugun abu akan kowa!

Yaku Yara ! Hikayar da aka ambata a sama na koya mana cewa mugun nufi koda yaushe yana zuwa da muguwar makoma da abin ki; kuma mun koyi cewa Allah عَزَّوَجَلَّ Shine mai karfin dayafi nakowa kuma mai karemu daga makiyanmu,kuma mun koyi cewa mugun nufi yana haifar da matsala ko matsaloli haka kuma suma Matsalolin, Idan Allah عَزَّوَجَلَّ yaso, Ana Cirewa Mutum idan yayi Tuba na Gaskiya daga wannan mugun nufin nasa. Saboda haka ku zamo Yara na Gari kuma kowa ya kudure a Ransa cewa: Bazamu

Saurara kokuma mugani ko Furta Mugun abu akan Dukkan Musulmi ba'.

*Ĥum to burākisī kādaykĥaynsunayn na bolayn*
*Achchĥīĥībātbolayn jab zabānkĥolayn*

Wannan yana nufin Zamu dinga gudun Laifin kowane musulmi, Dukkan abinda muka sani akan sa Babu wanda zaiji daga garemu, kuma idan wani ya gaya mana bazamu jiba. Zamu dinga yin Magana Kirkine akan kowa a tsarin da Sharī'aĥ ta gindaya.

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب　　صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد



www.dawateislami.net

# Daga Igiyar Ruwa Zuwa kan Cinyar Mahaifiya

## 4. Daga Igiyar Ruwa Zuwa kan Cinyar Mahaifiya

An Haifi Annabi Musa عَلَیْهِ السَّلَام lokacin da idan an haifi Jariri Namiji acikin BanīIsrāīl ake Kashewa don keta abisa umarnin Fir’auna. Mahaifiyarsa رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه p Ta saka shine acikin Akwatin Katako sa’anan ta saka shi acikin Kogin Nilu Saboda Tsoron Fir’auna, (A wata Riwayar ance ta Boyeshi har Tsawon Wata Hudu) Akwai Hanyar Ruwa ta canal [Karamar hanyar ruwa daga Babban Tafki] Daga Kogin Nilu tana Wucewa Kusa da Fadar Fir’auna; Kawai saiga Akwatu tana yawo Akan ruwa ta cikin canal. A Gefe daya kuma Fir’auna ne da Matarsa Āsiyaĥ رَضِىَ الله عَنْهَا (Wacce daga baya take karbar Addini a hannun Annabi Musaĥ عَلَیْهِ السَّلَام) Suna Zaune Suna shakatawa da jindadi kuma suna Fuskantar Canal na Ruwannan, Ana haka sai suka Tsinkayi Akwatu tana yawo akan



www.dawateislami.net

Ruwa sai suka yiwa Bayinsu umarnin dauko Akwatin nan sai ga Yaro Kyakyawa a cikin Akwatin. Dukkaninsu Fir'auna da matarsa Nana Asiyah رَضِیَ اللّٰہُ عَنْہَا Sunji Kaunar Jaririn nan a Zuciyarsu Nana Asiyaĥ رَضِیَ اللّٰہُ عَنْہَا Tace da Fir'auna :

قُرَّتُ عَیۡنٍ لِّیۡ وَ لَکَ ؕ لَا تَقۡتُلُوۡہُ ٭ۖ عَسٰۤی اَنۡ یَّنۡفَعَنَاۤ اَوۡ نَتَّخِذَہٗ وَلَدًا وَّ ہُمۡ لَا یَشۡعُرُوۡنَ ﴿۹﴾

***"Wannan Jariri Sanyin idanunane da naka ,Kada ka kasheshi, Watakilama ya amfanemu kokuma mu rikeshi a matsayin danmu – kuma basu sani ba.***

*[Kanz-ul-Īmān (fassarar Qur'an)]*

*(kashi 20, Sūraĥ Al-Qaṣaṣ, aya 9)*

Sun  Rikeshi a matsayin Dan Riko amma tunda shi Annabi Mūsā عَلَيْهِ السَّلَام Jaririne Sai aka shiga Neman Mai Shayarwa Amma kuma dukkan mai shayarwar da’aka samo Annabi Mūsā عَلَيْهِ السَّلَام Baya karbar shayarwarta, A bangare daya kuma Mahaifiyar Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام Kuma a Bangare daya Tana cikin Matsananciyar Damuwa saboda bata san Halinda Jaririn Danta yake ciki ba, Daga karshe dai sai ta Tura ‘Maryam’, ‘Yar uwar Anmnabi Musā عَلَيْهِ السَّلَام zuwa Fadar Fir’auna domin neman Labari A lokacin data lura cewa Jaririn baya shan mama sai Tace da Fir’auna : “Zan kawo maka wata mata ko watakila jaririn yafara ya karbi shayarwar.”

Dagan an kuma sai Maryam ta tafi da Mahaifiyar Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام Zuwa Fadar Fir’auna kuma a take da ta fara Shayar da Jaririn عَلَيْهِ السَّلَام Da farawa



www.dawateislami.net

sai gashi yana karbar Shayarwar daga wajenta. Haka nan, Mahaifiyar Annabi Musā عَلَيْهِ السَّلَام ta hadu da Danta da suka Rabu!

*('Ajāib-ul-Quran, shafi. 171)*

## Sunayen Mahaifan Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام

Yaku Yara Masu Albarka! Sunayen Mahaifan Annabi Musa Sune Yuhanz da Imran. Tarihin da mukaji Yana koya mana cewa Allah عَزَّوَجَلَّ yanayin abinda yaga dama ne Domin Fir'auna ya sa an yanka Jarirai Dubbunai Saboda Tsoronsa ga Jariri daya.Amma Cikin Ikon Allah عَزَّوَجَلَّ Fir'auna ne ya Raini Jaririn dayake Tsoro a Gidansa!Haka kuma mun gane cewa idan Allah عَزَّوَجَلَّ Yayi nufin Kariya ga Bawansa, Babu abinki dazai sameshi koda kuwa acikin turnukun Igiyar Ruwa,Kamar yadda Allah عَزَّوَجَلَّ Kare Annabi Musā



www.dawateislami.net

عَلَيْهِ السَّلَام Daga Igiyar Ruwan Kogin Nilu ya kuma Mayar dashi kan Cinyar Mahaifiyarsa عَلَيْهَا رَحْمَةُ الرَّحْمٰن.

*Tū nay kis shān say Mūsākībachāīĥayjān*

*Tayrī qudrat pay mayn qurbān Khudā-e-Raḥmān*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب        صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد



www.dawateislami.net

# ‘Yar Fir’auna Majinyaciya

## 5. 'Yar Fir;auna Majinyaciya

An ruwaito Cewa Mahaifiyar Annabi Musa رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه Ta saka shi a Cikn Akwati kuma ta jefa a Kogin Nilu. Fir'auna yana da'ya Guda daya kuma yana sonta matuka,kuma tana fama da cutar Leukoderma[1]. Firauna Ya nemi Shawarar Kwararrun Likitocinsa da kuma Matsafansa kan Yadda za'a magance mata wannan cuta: Sai suka ce masa 'Yakai Wannan Sarki Za'a iya maganin Cutarne Ta Hanya Daya 'Idan aka samu Yawun wanda aka tsinta a cikin Korama akayi amfani dashi a Wajajen da cutar ta shafa kuma a Tsakanin wata kaza da kaza kuma a Ranar da take da tsananin Hasken Rana!.

[1] Leukoderma kuma ana kiranta da vitiligo, Cutace da take sakawa mai ita Wani Farin Tabo ajikinsa da Hannaye idan yayi tsanani kuma yana kunbura Sassan jikin dan Adam kokuma Rashin Ji Idan an taba Mutum daga nan kuma Jikin Da kansa zai Dinga Zagwanyewa .

Da Ranar tazo, Fir'auna da Mutanensa Suka taru a Gabar Kogin Nilu a Tare dashi akwai matarsa Nana 'Asiya رَضِیَ اللّٰہُ عَنْہَا.

Karamar Hanyar Ruwa daga Kogin Nilu ta Ratsa ta Fadar Fir'auna, Kawai sai ga Akwati a kan Ruwa ta Ratso ta Igiyar ruwa yana Tunkudota sai ta Tsaya a Jikin wata Bishiya, Fir'auna yayi Umarnin a kawo masa Akwatin nan da sauri, Barorinsa Sukayi hanzari Acikin Kwale-Kwale dan dauko Akwati suka kawo ta gaban Fir'auna. Daga nan Ya Umarcesu da Bude Akwatin Amma Hakan Ya Faskara Haka nan Sunyi Kokarin Fasa Akwatin nan Sun kasa. Matar Fir'auna sai taga Wani Haske Yana Fitowa da Akwatin nan wanda ita Kadaice take ganinsa, lokacin da tayi Yunkurin budewa sai Akwatin ya bude a cikin Sauki Sai taga Wani Kyakyawan Jariri a ciki kuma wannan Haske Yana Fitowane ta Tsakanin Idanuwansa. Allah



www.dawateislami.net

عَزَّوَجَلَّ Ya Dasa Soyayyarsa a Zukatansu, Lokacin da ‘yar Fir’auna da debi Yawun Jaririn ta Sahafa a jikinta dai-dai inda cutar nan ta fata take a jikinta a take ta Warke daga Cutar. Sai ta Rungume Jaririn Da Tsananin Kauna, Wasu Daga cikin Mutanen suka ce masa Muna Da Shakka akan wannan Jariri ;Watakilama Shine Jaririn nan da aka sakashi a Kogi domin Tsira daga Garemu dan gudun Mutuwa , Bayan gama jin bayanansu sai Fir’auna ya Kudure a ransa cewa sai ya kashe Jaririn, Nana ‘Āsiyaĥ رَضِیَ اللّٰہُ عَنْہَا Tayi Nasara wajen Gamsar da Fir’auna cewa su Rike Jaririn nan su Raineshi. *(Tafsīr-e-Kabīr, mujallad. 7, Shafi. 580)*

## Abubuwa Hudu dake sa mummunan Karshe

Yazo Acikin *Sharḥ-us-Ṣudūr* Ceaw Abubuwa Hudu Na saka mummunan karshe:

1. Kasala Wajen Gabatar da Sallah
2. Shan Giya
3. Kin Biyayya Ga Iyaye
4. Cutarwa Ga Musulm

*(Sharḥ-us-Ṣudūr, Shafi. 27, Dār-ul-Kutub-ul-'Ilmiyyaĥ, Beirut)*

# SAKA GARWASHIN WUTA A BAKI

## 6. Saka Garwashin Wuta a Baki

Wata Rana Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام Yana Wasa da Itace a kusa da Fir’auna sai abisa Tsautsayi sai Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام Ya Kwalawa Fir’auna sandan nan aka! Dagan an sai ya kuduri Niyyar cewa sai ya Halaka shi, Nana Asiyaĥ رَضِیَ اللهُ عَنْهَا Tana Ganin abinda ya faru sai tace :

‘Ya Kai Wannan Sarki! Kada Kayi Fushi kuma kada ka samui Damuwa. Domin wanda ya aikata haka agareka ba kowa bane illa yaro wanda baisan mai yakeyiba ,kuma idan kana so zan Jarrabama shi Ka Tabbatar, Zan saka Gwal da Garwashin Wuta a kan Faifai Muga wane zai dauka , Sai Fir’auna ya yarda da a gwadashi, Lokacin da Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام Ya Mika Hannunsa Domin daukar Gwal sai Mala’ika ya ture Hannunsa Yana daukar Garwashin Wutar nan kawai sai yakai Bakinsa. Wutar ta Kona Masa

Harshensa Sa’an nan ya Furzar dashi Daga Faruwar Wannan Kuma sai Fir’auna ya Sauya Mugun Nufin sa  na Ganin ya kashe Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام.

*(Mustadrak, mujallad 3, shafi. 458, Ḥadīš 4150)*

*YāIlāĥī Tayrī ‘aẓmat Tayrī qudrat wāĥwāĥ!*
*Tayrīḥikmatmarḥabā! Tayrīmashiyyatwāĥwāĥ!*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب          صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Babu sauran Matsalar Yin Magana

‘Yaku Yara Masu Albarka! Ubangijinmu Allah عَزَّوَجَلَّ Ya Umarci Annabinsa Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام Ya Kira Fir’auna Zuwa Addini na Gaskiya Amma Yana Da In’ina Saboda saka Garwashin Wuta dayayi Abakinsa Saboda haka ga abin daya Roki Allah عَزَّوَجَلَّ Yazo Acikin Qur’ani ‘Musa Yace, Ya Ubangijina ka Bude min Kirjina, Kuma ka saukaka mini Lamarina



www.dawateislami.net

‘Ka kuma Warware Kullin daya ke a Harshena

‘Domin su Fahimci Maganata

‘Kuma ka Sanyamin Waziri daga Dangina

‘{wato} Haruna Dan uwana

‘Ka karfafi gwiwata dashi

‘kuma ka shigar dashi cikin lamarina

‘domin mu tsarkakeka da yawa, Mukuma Ambaceka da Yawa, Lallai kai ka kasance kana Ganinmu

‘{Allah} Yace : An Baka duk Abinda ka tambaya ‘ya Musa.”

*[Kanz-ul-Īmān (Fassarar Qur’ani)] (kasha na 16, Sura Daha , Aya 25-36)*

Addu’ar Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام, Ta karbu Allah عَزَّوَجَلَّ Cire masa In’ina sannan ya Mayar da Dan uwansa Wazirinsa

## Maganin Cutar In’ina

Domin Rabuwa da cutar In’ina mai yi sai ya karanta Wadan nan Ayoyi na Sura Daha kafa Bakwai tun daga Aya ta 25 zuwa 28 a bayan kowace Sallah, اِنْ شَآءَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ Maganarsa zata dawo daidai.

رَبِّ اشْرَحْ لِيْ صَدْرِيْ ﴿۲۵﴾ وَ يَسِّرْ لِيْۤ اَمْرِيْ ﴿۲۶﴾ وَاحْلُلْ عُقْدَةً مِّنْ لِّسَانِيْ ﴿۲۷﴾ يَفْقَهُوْا قَوْلِيْ ﴿۲۸﴾

## Kana son Shan Lemon Kwalba?

(An Gyara Jawabin da Periodical ta Kasar Pakistan ta Gabatar a watan June na Shekarar

2011)

Yaku Yara Masu Albarka! Kuna son Shan Lemon Kwalba? Idan amsar ku itace eh, To dan dakata! Ka karanta illolin da irin wannan gurbataccen Yanayi da Lemukan kwalba suke kawowa Sa'an nan kuma sai ka zaba ka gani idan zai anfaneka a duniya da Lahirarka. Danzaki {Sweetener} Shine babban sinadarin hada Lemukan kwalba kuma ana samunsu ne ta Hanyoyi guda Biyu kodai wanda aka Matso daga Sukari kokuma wani Sinari Saccharin shi kuma wani farin Danzakine wanda ya Nunka Sikari har sau 300 kokuma sau 500 zaki, idan kuma na sikarine shima ana Zubawa da yawan ban mamaki a karamar kwalbar lemo 250ml zaka samu sugar karanin chokali kamar bakwai a ciki.' *(Faizān-e-Sunnat, vol. 1, pp. 712)* Wadan nan Lemuka masu dan Karen zaki suna cutar da Hakoran mu da Kasusuwan Jikinmu kuma saboda



www.dawateislami.net

yawan sukari dayake cikin jininmu muna iya kamuwa da Cutar Zuciya da Cutar Fata kuma ga damar zama Dan Lukuti wato kiba marar Fasali.

## Saccharine-Gurbatarsa da Alakarsa da Cutar Daji

Hukumar F.D.A. ta America mai sa ido akan ingancin Abinci da Magunguna, ta karbi Korafe-Korafe akan Abinci ko Abinsha da yake dauke da sinadarin saccharine. A wani Bincike ya nuna cewa Karuwar cutar Sankara {Daji} Acikin Amerikawa tana da nasaba da yawan amfani da kayan ciye-ciye dake dauke da Sinadarin Saccharine. Saboda haka A Kasashe da dama an Hana Amfani da wannan Sinadari haka kuma Amfani da Sinadarin Saccharine yana saka Sankartar Mafutsara.



www.dawateislami.net

## Rubewar hakoran masu yawan shan lemon kwalba

A cewar wani bincike da aka gudanar kan haƙoran yara a shekarar 1992 a Burtaniya, an gano cewa Dasashi ɗin haƙoran kashi ashirin cikin ɗari (20%) na yara masu son shan lemun kwalba (wato kowanne yaro na biyar) sun Rube. An gudanar da wani gwaji a kan beraye inda aka basu lemun kwalba. A sakamakon haka, haƙoransu sun lalace cikin wata shida. A wani gwaji daban, an sanya haƙoran mutum cikin kwalbar ruwa mai 'cola', kuma ya lalace, ya yi laushi har ya dagargaje .

## Lemon kwalba yana ruguza hanyar narka abinci aciki

Ɗaya daga cikin sinadaran lemun kwalba shi ne, phosphoric acid wanda yawanci ake amfani da shi wajen cire tsatsa daga ƙarfe. Wannan sinadari yana



www.dawateislami.net

haddasa tsananin Zafin ciki, wanda ke rage gudun aikin tsarin narkar da abinci, har ya janyo rashin lafiya wajen narkar da abinci.

## Lemon kwalba yan dauke da Gas mai cutarwa

Lemun kwalba na ɗauke da iskar gas mai illa da ake kira, Cabon dioxide wanda ke haifar da kumfa da muke gani. Muna jin daɗin shan lemun kwalba saboda kumfarsu, amma waɗannan kumfa suna ɗauke da iskar gas mai guba da muke fitarwa lokacin numfashi. Shan wannan gas mai haɗari ta hanyar lemun kwalba ba dabi'a ba ce, kuma yana da matuƙar illa ga jikin ɗan Adam

## Wanda Yaci Gasar Shan Lemon Kwalba ya Rasa Ransa

A India, an taɓa shirya wata gasa ta shan Lemun Kwalba Wani Daga cikin masu gasa ya sha kwalba 8

shine ya lashe gasar, amma abin takaici ya rasu jim kaɗan bayan haka! Rahoton ya bayyana cewa yawan iskar carbon dioxide da ta taru a jikinsa ce ta haddasa mutuwarsa

## Alakar Lemon Kwalba da Kalolin Sankara {Cancer} Guda shida.

Kalar Baki ta Lemuna masu (sanforin Cola) Sunada sinadarin caffeine daya ke samarwa jikin dan Adam kuzari na dan lokaci daga baya kuma ya koma Ragwanci, Shansa da yawa da kuma Rashin bin ka’ida wajen amfani da caffeine Yana Janyo Raunin Kwakwalwa, da Saurin Fushi yawan Bugun Zuciya, Samun Hawanjini da kuma ciwon Ulcer.

A wani Karin kuma Ana samun tawaya ga yaranda Iyayensu suna shan Lemon kwalba fiye

da kima acikin irin abinda kan sami yaran nan kuwa akwai (Misali, a Haifi yaro dan Kankani kokuma a haifi yaro da ciwon hauka ko makanta kokuma a haifeshi da wani bangare na jikin sa a Shanye etc.) Da'kwai abin lura sosai wajen amfani da lemuka wanda suna musabbabin janyo kalar Sankara shida, Wanda kuma yawan sankarar ciki da Mafutsara Yawan ya wuce na da, Kuma yaran dake amfani da Lemon kwalba suna fitarda Calcium da yawa ta bayan gida {Rashin Calcium ajiki yana cutarwa ga kashin dan adam}

## Rashin Nutsuwa da Matsalar Numfashi

Domin killace Lemon kwalba ana saka masa 'sulphur oxide' ko 'sodium benzoic acid' kokuma a gauyasu baki daya sukuma wadannan sinadarai suna janyo matsalolin Numfashi, Kyikayi jiki da rashin



www.dawateislami.net

nutsuwa baya ga gurbatattun kaloli da suma suna da irin tasu cutarwar suma kuma na daga cikin abinda ke tattare a lemukan kwalba.

*Raĥūn mast-o-bay-khud mayn Tayrīwilā mayn*

*Pilā jām aysā pilā YāIlāĥī*

*(Wasāil-e-Bakhshish, pp. 78)*

## Sukari Gubace mai zaki

Ana amfani da sukari duk fadin Duniyar nan tamu kuma Jikin dan Adam yana bukatar dai-dai Gwargwado na sukari amma ba sai sukari fari ba a'a jiki kan yi amfani da sikarin dake cikin Alkama, shinkafa, 'ya'yan itace da sauransu, etc.Ba lallai bane shan farin sikari or Alewowi domin samun kwatankwacin sikari a cikin jiknmu, Hakakuma mutanen dake fama da Karancin sugar a

cikin jini {Low Blood sugar ko Hypoglycaemia} Suna amfani da sugar ne gwargwadon umarnin likitansu. A Ka'ida komai idan yayi yawa yana cutarwa, A yanzu idan muka lura zamu irin yawan sikari da muke dirkakawa kanmu abin a lura dashine Misali shan Lemon kwalba, da ice cream alewa mai bawo da marar bawo kuma dukkanin su fa babu abinci acikinsu kawai dai ana amfani dasune domin shakatawa da dan morewa Amfani tasu kuwa wata hanyace wadda kamar kana hakawa kanka kabarine da kanka. Babbar cutarwar sikari shine yan kara yawan Insulin a cikin jini shi kuma idan yayti yawa yana hana 'pituitary gland' [wani hormones ne dayake daidaita girma da bunkasar jikn dan Adam], wanda kuma zaisa Garkuwar jiki Rauni. Insulin yana karawa jiki damar Ajiye Kitse. Hakan kuma zai kara



www.dawateislami.net

nauyin jiki a karshe kuma a samu Kiba marar fasali {obesity}.

## Illar sukari

A lokacin tace Sikari daga Rake Dukkanin wasu abubuwan kara lafiya gada wanda jikin yake bukata dan bunkasarsa ana rabasu da rowan raken kafin busar dashi kamar su Vitamins, da minerals da ptroteins da Enzymes da sauransu. Saboda akace dukkanin abin da zamu kira sikari ko sugar baya tattare da komai na Karin lafiya ko na bunkasar jikin dan Adam sai dai yana tattare da abubuwan da zasu ruguza Na'urar narkar da Abinci a cikin mu, Irin wannan Farin siksri dayake kasuwanin mu bashi da wani amfani ga jikinmu sai dai zai iya zama kanwa uwar gamin a samuwar Sankara .Kuma daza'a lissafa adadin cutukan da sikari ka iya jawowa



www.dawateislami.net

na kai tsaye ko na hadin gwiwa da hakika an samu adadi mai yawa matuka. Sikari yana Raunata Garkuwar jikinmu sosai wannan kuwa bude kofa ne ga cutuka masu yawa  Yana taba adadin Gishirin jikinmu, yana janyo Rubewar hakora, yana saka Furfurar gashi, yana saka ciwon kai sa'an nan kuma yana kara yawan Kwalasterol {cholesterol} Yawan shan sikari yana nufin Ka hana Vitamin C shiga farin cell din jinika.Ta wannan hanyar kuwa ka Kassara Garkuwar jikinka da kanka!.



www.dawateislami.net

# Abubuwan da littafin ya kunsa


## MAFARKIN FIR'AUNA.................... 1

Excellence of Ṣalāt-'Alan-Nabī ﷺ ................................ 1

1. Mafarkin Fir'auna ................................................ 2

Menene Sunan Fir'auna na Gaskiya ?............................ 3

2. An saka Annabi Mūsā عَلَيْهِ السَّلَام A Cikin
Tanderu[Tukunyar kasa ta gasa gurasa] ........................ 5

3. carpenter ya zama kurma........................................ 7

Kada mu saurara kukuma mugani kukuma mufadi
mugun abu akan kowa!................................................ 9

4.Daga Igiyar Ruwa Zuwa kan Cinyar Mahaifiya ....... 11

Sunayen Mahaifan Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَام ..................... 14


5. 'Yar Fir;auna Majinyaciya ...................................... 16

6. Saka Garwashin Wuta a Baki....................................20
Babu sauran Matsalar Yin Magana...............................21
Maganin Cutar In'ina ...................................................23
Kana son Shan Lemon Kwalba? ...................................23
Saccharine-Gurbatarsa da Alakarsa da Cutar Daji .....25
Decay of teeth amongstpeople addicted to soft drinks......26
Soft drinks destroy digestive system .............................26
Soft drinks contain harmfulgas .....................................27
Wanda Yaci Gasar Shan Lemon Kwalba ya Rasa Ransa.27
Alakar Lemon Kwalba da Kalolin Sankara
{Cancer}Guda shida. ......................................................28
Rashin Nutsuwa da Matsalar Numfashi.......................29
Sukari Gubace mai zaki ................................................30
Illar sukari.......................................................................32

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَالصَّلٰوةُ وَالسَّلَامُ عَلٰى سَيِّدِ الْمُرْسَلِيْنَ اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ

## Help your child take interest in studies

The child who doesn't show interest in learning the glorious Quran or he lacks interest in religious education and Dars-e-Nizami, then recite يَا اَللّٰهُ يَا رَحْمٰنُ **101 times**, blow onto water and make him drink five times a day. اِنْ شَآءَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ he will take great interest in studies.




MAKTABATUL MADINAH
Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagran
Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan
UAN: +92 21 111 25 26 92 Ext: 1262
E-mail: translation@dawateislami.net Web: www.dawateislami.net